

Biri Sarkin Fada
Littafin karatu a sauƙaƙe - Mataki na 3
Hausa

Zuwa ga malamai da iyaye:

Kafin a fara amfani da wannan tsarin koyon karatu, dole sai ɗalibi ya: • San amon sautukan haruffan Hausa; • Iya gane kalmomin da aka saba da su.

Biri Sarkin Fada
Hausa Nigeria

Copyright © 2017, Enabling Writers Project -American University of Nigeria


http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/
http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye haƙƙin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su. ISBN

Grace Malgwi Writing Trainer/Collection Editor
Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa Hausa Language Consultants
Nas Yakubu Bloom Trainer
Story Writers Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi
Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0 Copyright: SIL International 2009



Gata nan gata nan ku.
Anyi wani gari can da nisa.
A garin anyi wani adalin sarki.
Jama'arsa suna sonsa.

Kwatsam sai aka yi wani baƙon biri.
Ana nan har ya zama sarkin fada.
Ashe birin munafiki ne.



Biri ya shiga zuga sarki.
Sonsa ya raba sarki da jama'a.
Hakan ya ɓata wa sauro rai matuƙa.
Shi ma ya shirya wa biri makirci.




Wata rana sarki ya gaji.


Ya shiga bacci.

Ya ce ka da a tashe shi.

Kwatsam sai ga sauro a ƌakin sarki.




Biri ya ga sauro.
Biri ya fusata.



Ya ɗauko takobi don ya kashe sauro.
Ya yi nan sauro ya yi can.
Kashe sauro ya gagara.

Sauro ya zauna a hancin sarki.
Biri ya kai sara.
Kawai Biri ya fille hancin sarki.



Biri ya bar gari.
Sarki ya zama marar hanci.



Haka sarki ya ci gaba da
mulki.

ALL CHILDREN READING: A GRAND CHALLENGE FOR DEVELOPMENT

USAID FROM THE AMERICAN PEOPLE

World Vision

Australian Aid

GLOBAL READING NETWORK